Ganin kamar ma kurma yazama yasa ta fara kaimai duka ta ko ina wanda bayaji sam, ganin tana bata mai lokaci kuma gashi jinshi yakeyi kamar zai mutu yasa ya D'an dagata Tareda keta kayan jikin ta ya fisgesu yanzu idanun shi sunrufe sai sambatu yakeyi ita kuma tana ihun neman ceto,

Wanda su Husaina najin komai kuma bazasu iya zuwa ba da gudu Hassana ta fita zuwa dakin momy wanda tayi sa'a tana zaune tana nafila kuma batajin ihun Sofia saboda dakinta da tazara da nasu,

Ganin shigowar Hassana a guje yasa ta sallame tana ke lafiya? " momy yaya zai kashe Aunty Sofia kije ya koremu,

Mikewa momy tayi jikinta narawa tafita hannun ta rikeda carbi,

Tana fitowa falon taji ihun Sofia, da gudunta ta karasa Cikin dakin tareda fara buga kofar uwar dakin " Abdul Rahman kabude kofar nan ko ranka ya baci kajini ko? Take fada Cikin fada wanda Sofia tanajin muryar ta ta samu ta zaburo tareda gallamai cizo a bakinshi dake Cikin nata ta dire tareda nufar kofar, ta bude ta, shigowa momy tayi tareda saurin kauda kai daga Kallon Sofia tayi saurin daukar towel ta jefa mata daurawa tayi tafita falon a guje,

Matsawa tayi gaban gadon da yake Cikin abin rufa iya kugunshi idanun shi a sama tun saukar ta , numfashin shi ya tafi tareda wani irin kafewa domin ya mugun shiga yanayin yana last stage na kwadaituwa da ita ta sauka, momy datake jin idan ta matsa sai ta samu Abin duka ta bugeshi yau koda ciwo kadan ne tajimai yadawo Cikin hankalin shi, taga ya kafe kamar gawa , tuni fadan ta ya koma ta matsa a tsorace tareda dukan shi kadan,

A matsanan cin tashin hankali,

"Abdul ta kirashi tareda bubbuga shi tanaja baya. Wanda ihun da tayi yasa gaba daya su Husaina suka fado dakin Har Sofia, dake tsorace, da dakin saidai ganin halin da Abdul Rahman ya shiga yasa taja baya tareda dafe kirji ganin shi kamar gawa ta zube zaune tana girgiza kai, Hassana ce tayi karfin hali ta dakko ruwa ko momy a daskare ta ke, ita ta bude tareda duddula mai su, wani dogon numfashi ya janyo tareda dagowa yana dafe Cikin shi yana juyi kamar zai kuma suma, da gudu momy ta matsa kusa dashi,

  Tareda dago kanshi ta dora kan kafar ta tana daidai ta nata numfashin jitayi kamar itama mutuwar zatayi domin tana yimai so mara misali, batason Abinda zai cutar da Rayuwar Abdul Rahman duk da ita kullum hada mata zafi yakeyi,

"Abdul Rahman meke damunka meyasa komai sai kadauke shi da zafi meyasa bakada hakuri akan Abun duniya kanaso kasani a Cikin matsala a rayuwata idan kabari wani Abu yasameka ko kasan ina sonka kuma ina son ganin farin cikin ka why kake garaje? Don't you trust your mother son?

Girgiza kai yayi tareda janyo hannun ta " momy kince bazan Aureta ba ita kuma tana guduna momy yazanyi , yafada yana Kara gyara rufar jikinshi Aliyar shi yayi nasarar sata tsakanin cinyoyin shi duk da hakan nayimai zafi, Amma dole ya boye erection dinshi a idanun ta, don duk rashin kunyar D'an halas dole yake barin wani Abun, Sofia mikewa tayi tareda barin dakin ganin y'anda duk momy ta damu su Husaina ma suna gefe suna kallo domin tsoron shi sukeji sosai don sun lura

Baya bukatar Susan meke faruwa haka momy, duk da su ba kana nan yara bane Amma kuma sunada kiyayewa momy ta dorasu akan hanyar kaucewa bincike akan Abinda bai shafesu ba, kuma sunsan koma meye ba hurumin su bane don haka tuni suka ware,

A zaune take a falon nasu ta hada kai da guiwa tareda jan numfashi, kusan rabin mutuwa tayi ganin idanun shi a kafe, that means I still loves him? Saidai tsoron shi da takeji batason Wani Abu ya kuma shiga tsakanin su domin baida sauki haukace mata yakeyi bana wasa ba,

Tsorata ta yakeyi ga katuwar sandar shadin shi,

Abdul Rahman daban ne a Cikin maza Allah yamai kira ta burgewa tareda daukar hankalin kowace Lafiyayyar mace wanda ita tasani, he is one in town,

Amma wannan rayuwar bazata iya da itaba dole ta Kara gaba bazata iya ba,

Momy ta hada mai ruwa a dakin ya tashi tareda daura towel ya shiga yayi wanka ta gyara musu gadon tareda jin tausayin shi tasani he is in need kuma tana ji jikin shi yq mugun daukar zafi alamar he is sick, kafin ya fito ta tafi kitchen ta yomai hade hade a ruwan tea na house remedy irin na mata da suka san kan rayuwa da wayewa,

A Al Adar ta hakan ba wani Abu bane Amma da yake macece mai riko da Addini tasan rashin dacewar Abinda yakeyi shiyasa ta tsaya tsayin daka take jajircewa akan tarbiyar yaranta,

Yasha tea din ya kwanta a dakin bai koma nashi ba, yanayi yana runtse idanun shi bayajin dadi sosai Allah yagani, zama momy tayi a gefen shi, " son kaje dakin ka mana, " momy barni a nan please let them go to my Room nan zankwana,

"Ok good night tafada tana juyawa tareda kashe mai haske, samun Sofia tayi ta hade kai da guiwa, ta rikota tace " let go daughter, binta tayi suma suka bita part dinshi suka shiga su duka, wanda tundaga falon Sofia ta shaida muhallin shi ne domin kamshin shi ne number one da yamata welcome, sai katon hotunan shi window size, ga wanda yana Abroad cikin shigar turawa katuwar jacket harda scalp a wuya da facing cap,

Yayi masifar kyau, batasan lokacin da ta zubawa hoton ido ba sai wani kuma da yake cikin manyan kaya yana Kallon Sama Abin burgewa, Ajiyar zuciya ta sauke, "how I wish you are not wicked, tafada tana zama, momy ce ta koma dakin ta kawo mata kaya ta saka batajin wanka ma zata iya yi domin haryanzu a tsorace take, momy want to talk to her Amma yanayin ta yasa dole zata bari gari ya waye tadawo cikin natsuwar ta,

Kwanciyar su sukayi suka barta a zaune batajin zata iya runtsawa Kallon ko ina takeyi a cikin dakin tana Kallon dukiya da hutun da ya taso ciki Abdul ya wuce da tunanin ta, ta ko Ina,

Har Asuba a zaune take,

D'an zaman da tayi dashi tun a Barrack ta san idan Asuba tayi yana fita masallaci don haka lekowa takeyi tanaso taga fitar shi, tana lekowa yana fitowa kuwa yanayi yana dafe kai ya nufo hanyar dakin nashi domin canja kaya zuwa masallaci, saurin boyewa tayi bayan labule har ya wuceta tayi dakinsu twins da gudu, Jakarta kawai ta dauka tareda hijabin ta a hannu, ta fita da gudu daga falon, she just want to leave this house anyhow,

Tayi sa'a tasamu mai gadi ya kewaya Kama ruwa domin yin Alwala,

Ta samu ta gudu, Unguwar kasancewar ta kamar GRA yasa bataci karo da kowa ba saida taga tayi nisa ta tsaya tareda saka hijabin ta tafiya tayi sosai batasamu Abin hawa ba, har gari yayi haske kafin tasamu taxi, tace ya kaita tasha, Jakarta ta bude she no's she have money inside, tafiyar minti talatin ya kaita tasha mafi kusa tayi

sa'a tasamu motar kd a layi kuma takusa cika ta ciro dubu daya ta mika mai ta shiga sahu, domin tasan yanzu ta tsira,

A hannun Abdul, hour daya da Rabi suka isa garin gwamna wanda motar soba ta nema a tasha ko ta barrack batabi ba domin batason duk inda zasuyi clash da Mr wicked,

A gefen Abdul kuwa yana shiga dakin yaga twins kwance bai kawo komai ba duk zuciyar shi tabashi tana dakin momy, kaya kawai ya canja kaya ya fita, saida momy ta tashi ta hada breakfast da masu aiki ta shiga dakin, nasu lokacin ko tashi basuyi sunyi sallar Asuba ba ta tashe su tana baya ina Sofia ita kota tashi ne? "Tashi sukayi suna murza ido, hasana tace kila tana bathroom, basu wani damu ba suka fita zuwa nasu dakin momy ta fita ba wani dogon tunani, saida suka hadu a dining ne suka fara tunanin something is fishy lokacin ita kuwa tayi nisa domin harta shiga Cikin garin nasu na soba gari mai tarin Albarka da kuma noma tareda mutanen kwarai,

Wani iska ta shaka mai ni'ima tana tunanin inama momyn ta nada rai da tasan itace gatan ta itace zata zamo Abokiyar shawarar ta rashin uwa babban tashin hankali ne a rayuwar ya'ya,

Tasan baba yalwa ba wani tarbar Arziki zata yimata ba amma batada zabi nan ne tushen ta Asalin ta kuma gidan ubanta ko mai wuya ta shirya rayuwa a ciki....

Matar Soja

[6/23, 1:20 PM] +234 806 628 8263: ..... A natse ya fito yanajin momy na tanbayar su " bazaku shiga ku fita ku nemo min Sofia ba ina zata boye a cikin gidan nan? Saurin matsawa yayi domin jin meke faruwa, kafin yayi magana Husaina ta

gudu dakin nasu ta duba da kyau, still bako walkiyar ta, gefen da Jakarta take ta duba taga bata nan, da sauri ta juya ta fita tana cewa " momy bata nan kuma harda hand bag dinta ta dauka,

Zabura yayi tareda fitoda idanun shi waje tuni yaji zafin da yakeji ya karu cikin tsananin tashin hankali "what are you saying??? "Yaya Aunty Sofia bata cikin gidan nan domin bata wuce daki ko falo duk mun duba bata ciki,

Da kanshi ya nufi dakin yana kwala mata kira " Sofy" Sofy " shiru baya yafito tareda fita kofar gidan ya nufi mai gadi yana kwala mai kira cikin tsananin tashin hankali, " gani Alhaji. " kaga wannan yarinyar ta fito dazu ko yanzu? "Ranka ya dade ba wanda yafita gidan nan yau da safen nan, don bayan masallaci sallar Asuba ba inda na daga,

Dafe kai yayi yana tuna tunda Asuba yashiga dakin shi ita bata ciki sai su twins, kenan ta dade da barin gidan? "I will this house, maganar ta tadawo mishi da gudu ya koma cikin gidan, momy ta rikeshi ganin duk a rude yake "son relax za a ganta kaga bawani dad'i kakeji ba ko,

Fuskar shi gwanin tausayi yace "how can I relax momy ta bar ni ta gudu momy tafada min zata bar gidan nan tunjiya Ashe she mean it,

Sakin shi tayi ranta a bace " yes now saikaji dad'i ai tunda zalamar ka taja maka kana kokarin haukewa yarinya kamar dole ba dole ta nemi gudu ba, wallahi zalamar ka tayi yawa baka Abu cikin hankali da natsuwa, now be happy she left the house kaje kayi duk Abinda kaga dama, rungume momy yayi yana jan numfashi "no baby please you are my supporter don't do that, karki karamin zafi akan wanda zuciya ta ke ciki bazan iya dauka ba " me yasa zata gudu menayi mata I love her ne sosai da bana iya controlling kaina akan ta taki ganewa momy soyayyar tace sanadi, kuka yafarayi kamar wani karamin yaro. Tuni momy ta hadiye fadanta, ta lura akan soyayyar Sofia jarumin D'an nata rago yake komawa,

Kannin shi ma tausayi yabasu seeing there brother crying for the first time, suma suka farayi, Dady ne ya fito cikin shiri ya zuba musu ido tareda tanbaya "lafiya kuke a haka meke faruwa? Sakin momy yayi tareda komawa wurin Dady ya rungume shi yana shashsheka kamar wani jariri "Dady she run away, ta tafi ta barni Dady why?

"Hmmm Abdul Rahman dama zataci gaba da zama a nan ne ba wani dalili inaso dama inji dalilin zaman nata a nan bayan momyn ka tace ba zancen Aure a tsakanin ku ta hana, yanzu tunda ta tafi saika yi shirin tafiya kaduna dama commander

dinku ya kirani jiya lokaci yayi don haka ka shirya katafi kawai yau ko gobe, daga Dady yayi yana share hawaye tareda jin zafi har cikin kirjin shi, "zantafi yau Dady yafada da kudurin zuwa ya cimmata a can, "Good, get ready Allah ya bada sa'a, Dady yafada kafin ya wuce ya barsu a nan, breakfast dinshi yayi ya bar gidan, Abdul Rahman kuwa dakin shi ya fada tareda shiryawa cikin sauri so yake kawai yaganshi a kaduna a kuma kusa da ita,

Samun shi a dakin momy tayi domin tasan Meke kasan ranshi, dauke take da tray ta Ajiye akan table dake gefen gadon, ta zauna tareda zuba mai ido yana shiryawa cikin sauri, "Son, come here, ta nuna mai gefen ta domin fuskar shi kawai tana iya isarda sakon zuciyar shi,

Zama yayi tareda zuba mata ido, "gani momy, "take it easy don't misbehave please, sannan my last advice to you, karka tsallake maganar baban ka this time around, domin duk da nagari dole yabi maganar iyayen shi, if you want to achieve in your life, follow the right part, shine akace bin nagaba bin Allah inji hausawan ku, karka bari baban ka ya kuma complain akan ka Abdul Rahman, idan kaci gaba da bijirewa Allah zai iya jarabtar ka ya hanaka Abinda kakeso, do you want to loose her? Girgiza kai yayi "then obey your father, go and make him proud son, sannan zancen Sofia trust me kaji zakayi farin ciki one day insha Allah, shiru yayi kawai ta hada mai tea yasha kadan domin bakinshi sam baimai dad'i,

Wayoyin shi ya kwasa tareda laptop domin yasan shi mai gida biyu ne no need ya kwashi kaya, kannin shi da momy na mai fatan Alkhairi ya bar gidan burin shi bai wuce ya ganshi a kd ba, motar shi yafada daya, ya tafi suna daga mai hannu momy na binshi da Addu'a tareda fatan Alkhairi tasan yana cikin tsananin damuwa, tayi murmushi tareda cewa "you will be proud my son,

Saida ya bar gidan suka koma ciki tareda daukar wayar ta number faruk ta nema sukayi magana, ta kashe tana fara'a,

Tuki yakeyi yana tunanin when zata gane tana wahalar da Rayuwar shi, yaushe zai samu dama ya mallaketa baki daya tazama a karkashin inuwar ikon shi batareda ta tsallake umarnin shi ba he want her under his roof bayason tazama karkashin inuwar kowa sai tashi,

Yaushe ne zata fara kulashi tabashi soyayyar ta like the first time, " you teach me how to love you and now am deeply madly in your love, and you are running away from me, why baby why?

A haka har Allah ya kaishi kaduna lafiya,

Sofia kuwa ta isa soba lafiya cikin gidan su tundaga hanya ta janyo idanun Al umma da basa gajiya da kallo, har ta isa wani D'an madai dai cin gida, ginin suminti ne irin na kauye, zuciyar ta na bugawa tayi Sallama, tsohuwar dake zaune tana kadi ta Amsa ba wata tsohuwa tukub bace saidai daga gani ta manyan ta,

Dago kai tayi fuskar ta cikeda mamaki da kuma Al ajabin ganin ta " Aa Safiya kece da safiyar nan ina zaidu shikuma? Zama tayi kanta akasa ta gaida ita, tareda tanbayar bayan rabuwa, " yaya na kaduna, nikadai Nazo tafada kanta akasa tana kuma mamakin laushin tsohuwar yanzu domin ta iya fitina matar,

"Ina fatan lafiya ko? " lafiya kalau Nazo dubaki ne kawai tafada tareda boye Gaskiyar lamari, gwara da kikazo ai domin D'an gin mahaifin ku sun sani gaba wai nasa kunbar gida sunzo gidan nan yafi sau Ashirin ni bansan me suke nema dani ba, bani nace zaidu ya dauke kiba shi yaga zai iya tunda bani na haifeku ba,

Amma tunda kin iso bari insamu Almajiri ya nemomin buba yazo gaki kindawo su sakarmin mara inyi fitsari,

Almajirin ne yayi Sallama itadai ko tub batace ba zuciyar ta tayi nisa bata ko jin surutan baba yalwa, wane hali yake ciki? Me momy ke tunani yanzu, shin ta kyauta wa momy kuwa? Matar bata can can ci haka ba, Amma dole ce tasa tayi hakan domin tsira da mutuncin ta da kuma tseratar da kanta daga oga mugu,

Baba yalwa tace "kai D'an malam jeka gidan malam buba mai buzu kace yazo inji yalwa yanzu,

Fita yayi ita kuma ta mike tareda Kallon gefen dakin su wanda yake na mahaifiyar su ta ji wasu kwalla sun ciko mata batada wani wayau ta rasa iyayen nata Amma tasani tana matukar kewar ta tana bukatar su a yanzu rashin iyaye babbar matsala

ce, dakin na nan komai yanda suka barshi, saidai kura don haka ta cire hijabin ta ta bude tsohuwar adakar babar su ta ciro zanin ta ta daura akan doguwar rigar jikinta, tafara clean up,

Hour daya gyaran ya dauke ta, ta tsabtace komai har zanin gadon dake kan gadon karfen mai rumfa ta wanke, baba yalwa na Kallon ta tace "in kin kammala taho ga dambu na Amso miki da zafin shi kici.

Abin yana bata mamaki ganin canjin tsohuwar, zuwa tayi ta zauna taci sosai domin akwai yunwa a jikin ta, don bata karya ba,

Sallamar buba tasa ta mike tareda Amsawa tana gaida shi domin shigowa yayi mai tsaye, "aa maraba da Y'ar gidan baba, Safiyatu kece? "Eh baba nasame ku lafiya, "Alhmdulillahi Y'ar Albarka, "Allah ya tsareku keda D'an uwanki Allah ya Albarkaci rayuwar ku baki daya, ai shi ko shekaran jiya yazo nan da bindigar shi da kakin shi, yazo munyi magana akanki,

Kallon buba tayi kawai batason jin zancen yaya Zaid baya sonta sam,

Shigewa tayi dakin data gyara domin hutawa, tabarsu anan suna fama domin magana yake fada mata "kiyi kokari ki gwada mugun halinki kisa yarinya ta gudu kinji yalwa wallahi kinsan halin D'an Uwan mahaifiyar ta, yanzu ma zankirashi infada mai nasan inda ya'yan kanwar shi suke domin saboda zaidu naki fada don yafada min uzurin shi, Amma yanzu ni bazan zama dattijon banza ba shima zaidun kiran shi zanyi inji dalilin da bayaso yasan Y'an Uwan mahaifiyar tasu,

"Nidai buba ka fitine ni a baya kace na kori ya'ya yanzu kuma gasu duk sundawo sai a sake min mara haka nan gidan ubansu ne ni mai gadice ko yau sukace infita fita zanyi don banda gado tunda ban Ajiye ko kyanwa ciki ba, "shiyasa bakisan darajar ya'ya ba tunda bakisan zafin nakuda ba, "Wannan kuma daga Allah ne buba Amma yara dai nayi iya yina fada ne ajini na yake ba wanda zai iya canjani.

"Allah ya yaye miki. Ya fita Abinshi ta bishi da Mita, kaima da kake kanjn uban nasu in banda D'an banzan iko uwar me ka tsinanawa rayuwar su gwara ni ma na dafa sunci, tafada tana tsaki,

Abdul Rahman na isa block ya fara nufa domin sa ran ganin ta, saidai wayam bakowa kota dakin nashi baibi ba ya kira Zaid , ya dauka "aa oga Abdul yau agari? Ina sister? Itace zantan bayeka kota dawo nan dazu? "No ni yanzu na fita gidan ma a nan nakwana bata zoba,

"You are such a bad brother you are too careless zaid yaza ayi iaia fada maka banganta ba kai ko ajikin ka, "ai nasan Sofia bazata bace ba inba sace ta akayi ba indai da kafarta ta fita bazata bata ba, katse kiran yayi yana godewa Allah da zaid baya kusa dashi yau da ya bubbuge shi saboda takaici,

Rasa Abunyi yayi tareda juyawa motar shi yabata wuta ya nufi block din da yasan zai samu James, tsawon rayuwar shi a barikin ba rayuwan shi da sanin inda friends dinta ke rayuwa Amma yau dole ya neme su, yana fakawa james nafitowa daga dakinshi da guntun wando, ya tsaya yana Kallon Abdul domin yanda labarin bazai dawo office dinsu ba Arzikin yaci uban nada very soon zai basu odar idan yafito short service don haka dole yafara obey, don ko banza bakin rijiya ba wurin Wasan makaho bane, jiki na rawa ya matso yana Sara mai bakinshi har kunne,

"Aa oga Abdul wel done wo na yerstady I hear the good news congrats, "tanks yafada fuskar shi ba wani wal wala, "please were is your friends? "Who? Blessing and co. "Oh your babe friends, now am with blessing, ya kwala mata kira ta fito da towel a jikin ta tana mika Alamar an dinke, shegiya bariki,, sosa kai yayi " you see now na bleesing I dey follow because sofy don pass my power na your babe, ita kuwa tana ganin shi jikinta yafara rawa domin bazata taba mantawa da dukan tsiyar da sukasha ba har gobe akwai tabon a jikinta, kokarin juyawa take ya hangota ya ce "wait please, cikin sanyi domin ya karanto tsoro a bayyane a fuskar ta, matsawa yayi tareda csaka hannu a pocket "please forgive me nasan nayi muku ba daidai ba, ina so insani ko Sofia ta dawo nan yau kunganta?

Girgiza kanta tayi jiki NA rawa " no mundade bamu ganta ba inmun kira ma bata daga mana waya ma, "Hmm were are the rest? "Suzanne taje porthacout zubaida na cikin gari nikadai ce a nan,

"Please akwai inda kike tunanin zata iya zuwa? Shiru tayi nadan lokaci tace "I think there village, "ina ne? Yafada jikin shi na rawa "I think Soba, yes soba,

Dariya yayi karon farko tareda riko hannun ta "tank you friend, because yanzu ke friend dina ce Nagode sosai, you no ina mugun son kawarku ne shiyasa kukaga ina jin haushin ku I thought tana bin maza like you All do, a she am mistaken, murmushi yayi yana tuna shine ya karbi budurcin ta, tuni blessing ta saki jiki tareda fitowa ta tsaya tana Kara fada mai more About Sofia what she likes and what she hates, "you are lucky to have her she is special unique and wonderful lady, "I no friend I no, but you no, yafada Cikin damuwa "she hates me now, zaro idanu bleesing tayi "how why what happened?

Dayake kunya bata ishe shiba yace because I took her virginity she is mad she is angry she leave me for that she hate me, dariya Bleesing tayi "at last you did it, to Mrs ta Sofia wow naso inganta kuwa gaskiya na jinjina maka, bata rai yayi "bansan cewa she is virgin ba shiyasa I forced myself, dafa shi tayi "Sorry friend saboda ka zo kana zaginta ne tun farko she is willing to sacrifice that just for the sake of your love, kaine kasa tafara tsanar ka Amma I no Sofia tana sonka sosai munyi fama da ita akan ka har fada takeyi damu,

He relax and listing to her story da irin gudun samarin ta da duk Abinda yakewa james dariya murna farin ciki duka suka hadu mai,.....

Matar Soja

[6/23, 1:20 PM] +234 806 628 8263: 59&60..... Cikin tsananin farin ciki yabar wurin tareda ciro rafar kudi masu kauri yabata, blessing kamar tayi hauka saboda farin ciki yau Mr Arrogant ya bata kudi yayi hira da ita, soke kudin ta tayi tana cewa " he is not that bad. Ta manta da narkar su da yayi kudi sun goge tabon a yau, James ma yasamu nashi sai ihu yake yana zabga yabo, ya Kama hanya har ya shiga motar shi yana niyyar daukar hanya kiran momyn shi ya shigo, dagawa yayi fuskar shi cike da fara'a yace " my momy my sofy loves me , kawarta tafada min

yanda take sona yau, " ina kake yanzu? Momy ta tanbaye shi, " ina Cikin barrack yanzu zantafi soba,

"Abinda nafada maka kenan ko? Amma nafada ma kabi umarnin Dadyn ku ko,? "Momy ina so inje inganta friend dinta tace min kila tana can. "Or you are not even sure? So listing to me very carefully, karkaje wani wuri ka wuce kafara service dinka kafin ka yi wani rashin hankalin. Bata rai yayi tareda rage murya " haba momy karki hanani kibari inje inganta don Allah, " Abdul Rahman karkaje ko ina kabarmin komai a hannu na nasan me nakeyi ai don haka follow my instructions in kuma bazaka biba kayi yanda kaga dama zan cire hannu na kuma baka ba Sofia har Abada and believe me zanyi hanyar da zata Auri wani kana gani,.

Please momy don't do that,zanbi maganar ki, yafada cikeda sanyi kamar wani maraya, ya datse kiran he really want to go and see her, Amma bayaso yarasata baki daya yanaso ya tabbar lafiyar ta da kuma ja mata kunne akan ta kulamai da kanta kafin yadawo, watannin nan da zaiyi zasu zomai ne kamar shekaru masu tsawon gaske har ya fara tausayawa kanshi bayajin zai iya kwana biyu baisata a ido ba,

Haka yaja motar jikinshi a sanyaye ya nufi block dinsu, Zaid yasamu ya dawo, ya nufi dakin shi, suka gaisa kanshi a kasa " please help me and take care of her please, kaje kaga mun lafiyar ta find out if she is Alright don Allah brother, harda hade hannu yana rokon shi, dariya zaid yayi "Hhhh gaskiya sister tayi kokari sosai na riko zuciyar gwarzon maza mai tsantsar ji da kanshi. " bazaka gane bane tayi mun mugun kamu ina sonta fiyeda kaina Ita dutse ce mai matukar daraja,

"Don't worry gobe zan shiga soba insha Allahu, nasan ma she is save, kuma trust me ba Abinda zai faru sofy is yours,, tashi yayi ya rungume shi tareda Kara bashi Amanar ta ya fita hada ina shi ina shi yafara yi kafin yaje office ya karbi duk takardun da zai bukata,

Ya wuce cikeda damuwa da kuma yiwa kanshi fatan Alkhairi akan Sofia, saida ya kuma kiran momyn shi ya Kara rokon ta taje ta nema mai Auren ta bayason ya rasata, tace yaje Allah yasa Albarka ya kuma tsare,

Sofia a ranar baccin ta tayi a gadon su hankalin ta kwance bayan taci tayi nak,

Ba Abinda take tunani sai momy kafin ta kwanta saida tayi plugin wayar ta a caji domin a mace take saboda rashin komawa kanta da takeyi,

Domin batason daukar wayar kowa,

Da safe data tashi kuwa ta kunna ta wanda tafara cin karo da tex msg daga Mr AA, " I love you Sofia, kisa wannan a zuciyar ki ni Abdul Rahman nafi kowa sonki bazan iya Rayuwa baki ba , for the first time am scared very scared to loose you, I don't want to loose you my life be mine for ever please karki kula wani namiji idan bana nan ki kula inada kishin ki kamar inyi hauka so nake na mallake ki, ina so inganki a karkashin inuwar iko na, I want to see you as Mrs Abdul Rahman Abdullah, tank you baby Nagode for protecting your virginity for me tank you for the best gift ever, kinbani the most precious thing ever, tank you for loving me, ni mai sa'a ne nasamu mace irinki I can't wait inganki as mine completely, please continue loving me don't leave me, pray for me infito lafiya,

At last ya rubuta

Love you future bride,

Sakon ya isa har kasan zuciyar ta yanzu ne take matukar jin tausayin shi, yanzu ne duk wani susucewar shi da kuma damuwar da ya shiga saboda ita tafara dawo mata, she can't believe itace yakeso har yakewa kuka, bazata manta yanda yake son makalewa a jikinta ba, kirjin ta takalla ta tuna yanda baya musu da wasa tareda irin budurin da yayi dasu ranar da ya barke ta, kasan ta tashafo tana dariya " you take it All AA you make me cry you are wicked you are Arrogant, but I still love you, I no you wrong kuma har gobe bana fatan ka kuma samu na I wanted to be your wife for ever but ka tsorata ni kafi karfi na.

Sai da ta karya ta kira momy, wanda tana dauka tace "daughter na kintuna dani? " sorry momy don Allah karkiyi fushi dani I no am wrong, " you are not, karki damu. Hakan ya nuna min kinsan Abinda ya dace ke mai tarbiya ce domin da wata Y'ar ce biyewa son zatayi Amma ke kin nuna mutuncin ki yafi soyayyar da kike mai,

Kanta a kasa kamar momy na ganin ta tace " am feeling guilty momy wallahi. " don't I understand, kuma kijira weekend zamu shigo soba muda twins harda Dadyn su zamu zo neman Aure tareda sada zumunci insha Allahu,

"Ok momy Allah ya kawoku tafada cikeda murna, domin bazata taba mantawa da wa'innan mutanen ba basuda kyama ba wulakanci sam a rayuwar su sunsan darajar D'an Adam, don haka bazata ce komai ba, Sallamar zaid yasa ta hade rai, taki

kuma tashi bare ta leka waje, komawa ma tayi tayi kwanciyar ta a gadon unman su, tanajin yana zuba da baba yalwa, tace mai tana ciki,

Tasowa yayi tareda bude labulen ya zubawa dakin ido tareda shigowa da katuwar akwatin ta da kuma jakar shi ta rataya wa, " oh wato ni ake kyalewa sister saboda ansamu masoyi ko,

Kamar tana jiran shi ta zabura tafara hawaye " wallahi yaya sai su Umma sun tanbaye ka idan ka mutu domin baka rikeni Amana ba domin da kana sona bazaka bari ya tafi dani ba

Dariya maganar ta tabashi wato idan yana wuri tanajin yin dad'in shagwaba, " oh my god Sofy keda kikabi mijin ki ni ina ruwana, "kuma naga ni ba a taba fadamin komai ba akan Abdul Rahman , kina boyemin damuwar ki bansan komai ba ni kin kyauta min kenan sai dai inji labari a inda banyi tunani ba?

In fushi ne nine zanyi dake I thought na isar miki komai ni mai share miki hawaye ne, Amma sai kika boyemin, nine yakama ta insan damuwar ki Sofia Amma kinboye min komai, matsawa tayi kusa dashi "sorry Yaya bazan iya fada ma ina son wani ba, Amma da ne yanzu nadaina sonshi. tafada tana cuno mai baki, dariya yayi sosai, "Allah, naji wannan, saboda ke kamar zaiyi hauka sister, you are lucky, Abdul nasonki sosai, yatafi NDA ya barmin Amanar Amanata, tareda zafafan sharudda tareda rokona,

Dariya tayi tasan haukar Abdul , "ga kayan ki nan i no bakizo da kayaba yafada min gudu kikayi, shiru tayi kawai Amma ta lura Yayan ta kamar baisan rashin dacewa ba, "yauwa sister brother din Umma da baki sani ba zai shigo nan zamu ganshi , I can remember duk da banda wayau sosai Umma na yawan maganar shi lokacin bai cika zama bane tafada min yana sonta sosai haka suka tashi like me and you ya mata Alkawari zai kula da ita kuma rai yayi halin shi, lokacin da yadawo Nigeria yazo soba lokacin munbar nan baba buba yafada min cewa ya yita zuwa cigiyar mu bai samu ba,

Dariya tayi domin tana son taga koda mutum daya ne da sunan dangin Umman su, don haka she is eager to see him,

Kwanakin sunzo mata cikin jin dad'in tareda tsananin kewar Abdul Rahman, wanda yanzu take dada yarda shine ita itace shi, saboda rashin ganin shi kamar mai ciwo tazamo, gashi baya waya saboda dokar inda yake service,

Wanda a wurin Abdul Rahman yafita matukar damuwa he is missing her like hell a wahalce kwanakin ke zuwa mishi yakasa sabawa da rashin ta, baisan y'anda zai yi watannin bata ba.

Gefen su momy shirye shirye sukeyi sosai na zuwan su soba wanda yazama dalili biyu,

Tana jin dad'in zaman ta ba wani takura ko tsangwama tanada kudi Abinda takeso takeci itada baba yalwa wanda ita kanta zaman Sofia yasa tayi shar Cikin kwanaki, yanzu tana communicating da friend dinta, Sunyi hira da blessing sosai wanda take bata labarin irin Alkhairi da Abdul yayi mata saboda har bata kudi yayi masu yawa su raba itada su Suzanne, wanda duk sunyi mata godiya suna mata tsiya domin blessing ta shafa musu labari,.

Zubaida tace "welcome to the team friend kema kinzama Y'ar hannu, " Allah ya kyauta, wannan ai kaddara ce katuwa wallahi mace nabin maza, kuma da kun hadu da gwarzo irin nawa bazaku kuma marmarin bin wani kato ba,

Meye fun a cikin sex, wallahi wahala ce, dariya zubaida tayi "gaskiya kibani labarin irin cinda Arrogant ya miki da kike tsoron sex,

"He is Arrogant even in bed bansan irin wahalar da nasha ba, but to cut the story short, harda stitches, zubaida tayi dariya kamar zata suma, saboda mugunta she wonder how huge mr Arrogant is da har yajanyo mata dunki kamar kwarya,

Ranarda su momy zasu iso kuwa da kanta ta dage ta hada musu dishes tayi waya da su twins yafi sau goma kafin su iso, wanda suna isowa itace tafara tatbar su domin wurin ta suka fara zuwa, baba yalwa ma tayi musu maraba, harda faruk Akazo, wanda suna zuwa ba dadewa zaid ya iso tareda malam buba, wanda Dady

da kanshi ya gano cewa Sofia Y'ar shi ce. Yar kanwar shi, tun basu karaso gidan ba, don haka cikeda farin ciki da kuma tsantsar kaunar Y'ar uwar shi ya kalli momy dake zaune gefen shi a motar yace "Aisha Abinda ya tsaya a zuciya ta ban bayyana ba ya zamo gaskiya a she,, " Mene ne? Ina ganin Yaran nan Yaran maryam ne kanwata da nake yawon zuwa nema Ashe Sofia yata ce Ashe kanwar Abdul ce, Ashe bayan soyayya ta so akwai ta jini a jikin su, Ashe boyayyen Al amari ne Allah ya boye da yakai Abdul Rahman rayuwar Sofia har yau gashi Cikin sauki nagano hakan,

Momy ma cikeda farin ciki tace ya kayi ka gano hakan Dadyn twins, kofar gidan ya nuna mata tareda cewa "indai nan take to yatace domin kamannin ta sun nunamin ita jini nace tun farko Amma na kawar domin Akwai mutane dake Kama, Sofia is just like my sister, "Kagani ko kaddara ce ta janyo komai, wato komai MUK'ADDARIN Rayuwa ne haka Allah ke boye Al amarin shi inyaso.....

Matar Soja

[6/23, 1:20 PM] +234 806 628 8263: 61&62..... A katon tsakar gidan aka baza tabarmi, baba yalwa ta tarbesu jiki na rawa, baba buba ma yazo gidan Sofia kulewa tayi dakin Unman su ita da twins sunata hira, so take ta tanbaye su labarin Abdul Amma ba hali tanajin kunyar su musamman idan ta tunada yanda aka yi rabuwar karshe itada shi, tasani itace a cikin jin kunyar Al amarin shi ko ajikin shi, kiran su akayi suka fito dukan su, tana cikin simple Adon ta sanye da hijabi, mugun kunyar momy takeji ko hada ido bata iya yi da ita, ta lura da hakan yasa tace " come closer daughter, gefen ta ta koma ta zauna, baba buba ne yafara Addu'a tareda godiya ga Allah, yayiwa iyayen su Addu'ar samun Rahama, wanda mutuwar ta dawo kamar yau akayi ta a gidan domin ba Abinda yake fada sai, "Malam isa ya shirya ne da ita mahaifiyar tasu Maryama domin kai ziyara wurin dangin ta Allah ya dauki ransu wanda badon da tsawon kwana ba Yaran ma bazasu rayuba,

Amma cikin ikon Allah yau gasu masha Allah, lokacin bayan rasuwar su naso inrikesu ita wannan fitinanniyar tace ai tana nan abarsu a gaban ta, wanda banda masaniyar wace rayuwa sukeyi, kuma kuskure na shine rashin sa ido akan Al amarin su, har takai ga wannan yayi fafutuka ya kai matsayin nemawa kanshi aiki har, ya dauke Y'ar uwar shi ina nan duka bansani ba, Alhaji Abdullahi naji dad'in haduwar mu a yau domin nasani sanya idonka akansu sai yafi nawa domin ni banda karfin da zanbawa wannan doka taji,..... " buba baka sona da zaman lafiya tundazu ba Abinda kake nema sai fitina dani kana neman lakato laifi kota wane lungu ka lankaya min to ta Allah bataka ba ai naga inda Amana kai mai sanya ido

ne akan Rayuwar su Amma tunda ubansu yabar duniya kwarar gero baka taimaka mana dashi ba kuma ni din nan fitinanniya idan na nema tareda su nake cinyewa bantaba hana musu ba har suka bar gidan nan.

"Toh Alhmdulillah ya wuce wannan yanzu.

inji Dady, "yara sun girma da ikon Allah gasu lafiya kalau, Zaid kayi kokari sosai wajen tsayawa Rayuwar Sofiya, tundaga kulawa iliminta tarbiyar ta kana namiji, dole injin jina maka, Allah kuma yasaka maka da Alkhairi, Sannan a rayuwa duk Abinda kuka ga ya faru akwai sanadin shi, MUK'ADDARI ne rubutacce hukuncin ubangiji ne don haka kar muyi shishshigi a Al amarin ubangiji, Allah yasa mudace,

Baba buba yace "Ameen Alhaji, kanshi a kasa, daman haka rayuwa take mutane basa tunanin ya kamata sai in lokaci ya kure, lokacin da taimakon ku bazai Amfani mutum ba sai kaga suna nadama mara amfani, kutaimaki mai bukatar taimako a lokacin da yake cikin tsananin bukata, ba sai lokacin da yafi karfin Abun ba.

Sunci sunsha Anyi hira sosai ta bayan rabuwa, momy tafi kowa farin cikin sanin cewa Sofia Y'ar kanwar Dady ce, tana son yarinyar sosai har cikin zuciyar ta. Wanda ta nemi su juya a tare da ita, Amma zaid ya bada uzurin gwara su koma kaduna domin soon zata zana jarabawar kammala karatun ta na diploma,

Wanda suka Ajiye agreement tana kammala wa zata koma Fct,

A gefe suka koma suka zanta tsakanin ta da momyn ta, "Daughter hope baki fadawa kowa Abinda ya faru tsakanin ku da Abdul ba? "No momy tafada kanta a kasa domin tana jin kunyar Abun, "karki damu karkiji kunya, bakiyi laifi ba bakida laifi ko daya kinji, ki kammala exam ki dawo Fct ina jiran ki kinji, trust your mother, ko ni ba maman ki bace? " momy nace ke tafada tana rungume ta tsam, dad'in Abun takeji sosai yau itace tare da d'an gin maman su kuma wai Dady is her Auncle, wani irin fara'a ne ke bayyana a fuskar ta idan ta tuna da cewa Abdul Rahman sun hada jini, she can't believe that, lallai wanda bai yarda da kaddarar rayuwa ba yayi hasara, bata inda bata juyawa. Inta kalli yanda aketa faman hira Abun yana matukar burgeta, yaya Zaid tuni yaja su twins sunyi waje shida faruk, mikewa tayi tabisu itama,

Tabar momy dady baba yalwa da buba,

Samun su tayi tsaye a jikin motocin nasu manya da sukazo dashi, wainda suka dauki hankalin mutanen Unguwar sosai,

Husaina dake makale gefen Faruk tace "nidai muje mu zagaya inga gari, kauyen ya burgeni sosai gashi babban gari,

Motar da Faruk ya tuko suka shiga suna baya su uku shida faruk suna gaba,

Sai tsiya yakewa Sofia "Amaryar officer yadai, yau naga wadda ta rikita min my Arrogant and classy friend,

Dariya kawai sukeyi su twins na Kara bada labarin haukar da Abdul din ya rikayi, "Hussy kintuna ranada ya hada waya da TV, Hmm ai guduwa mukayi ranar yaya kamar mahaukaci, gaskiya yaya bala'i ne kishin shi yayi yawa, zaid ma nan ya rika bada labarin y'anda ya rika kiran shi yana mai fada in sun fita itada kawayen ta, sunyi dariya sosai har suka gama zagaye garin suka dawo, lokacin su dady sunfito ana shirin tafiya,

Ya kira Zaid a gefe, "kaje ka shirya kasamu D'an uwanka a NDA kaima duk da you are late Amma na nemi Alfarma, zaka iya jona su, zaid kamar ya zuba ruwa akasa yasha don murna, , don haka tare suka wuce kaduna shidasu momy Sofia tace sai weekend zata tafi,.

Sun Ajiye mata kayan masarufi Kala Kala, tareda kudi kafin su wuce wanda harda su baba yalwa sun samu nasu da buba, tayi kukan farin ciki, tasan Auren ta da mahaifinsu MUK'ADDARI ne tunda sundauki shekaru basu haihuba ya Auro mahaifiyar tasu wanda daga zuwan ta ta samu ciki, Allah yagani tana son haihuwar Allah bai bata ba gasu kuma yau sanadin su tasamu Alkhairi, karike D'an wani da Amana bakasani ba wata rana ko shine zaiyi maka rana,

Akwana atashi ba wuya Sofia na cigaba da fafutukar ganin ta kammala karatun ta cikin natsuwa ta tattara ta koma kaduna tana waya da momy dasu twins wanda tana matukar kewar mutane biyu a yanzu wainda sunkwashe kusan wata na biyu a NDA batareda ta jisu ko waya dasu ba, Abdul da yaya zaid, tagama yarda Abdul Rahman Rayuwar tane, tasani akwai bond na jini gana zuciya wanda idan ta zauna tayi tunani tasan tsananin kaddarar haduwar su yakaishi bariki, duk gwagwar mayar Rayuwar tasu yafaro ne da MUK'ADDARIN haduwar su wanda Allah ya hukunta,

Tana jin zafin faruwar Abinda ya mata abaya Amma yanzu sabuwar soyayyar shi ta goge komai, she is missing him, domin ko dawowar ta bariki dakin shi ta tare nan take kwana nan take komai, ba Abinda take gani sai memories din soyayyar ta dashi ta wahala, sometimes zata kalli kofar ta tunada ranarda ya kulle ta a ciki,

Ya tafi Abuja dariya takeyi,

Idan ka ganta zakasan Batada wata damuwa a tattare da ita tana karkashin inuwar kulawar Dady kudi kafin su kare wasu sun shigo, bayason zaman ta kaduna yaso ta koma Fct ya nema mata wata makarantar Amma ta nace tanaso ta gama course din da ta fara,. She looks more pretty more elegant and more classy duk wanda ya kalleta sai ya tabbaar da ta fi karfin raini, momy har rokonta tayi ko akawo mata mota da driver tace " momy na gatan zaiyi min yawa ku bari in kammala indawo sai ku yi min duk Abinda kukeso Nima na matsu bandawo kusa da kuba, "toh Allah ya taimaka daughter,

Tana zaune tana nazarin littafan ta a dakin AA domin ta zamo mai daki biyu,yanzu tafi maida hankali sosai a harkar karatun ta fiye da lokutan baya da yawo ke cinsu, su Suzanne suka shigo, duk sun rage yawo da kuma rawar kai, zubaida ce ta ke kuka wiwi kamar Anyi mata mutuwa. Tana shigowa ta zube jikin Sofia, "subuhanallah, ya akayi Zuby? Blessing ce tafara fada " na that her bastard boyfriend, can you imagine ya bata kudi ta zubarda ciki saboda bayason haihuwa da ita, yace ta cire suyi Aure After she did it yanzu munajin labarin yana can yana daura Aure a kauyen su,

Suzanne ce ta kalle Sofia "why hausa people they do like that, bayan sun gama cinye ya'yan mutane sai sugudu kauye suyi Aure,? Bubbuga bayan Suzanne tayi saida tayi shiru kadan tace,

"Bazaku gane ba Al Adar mu tanada banbanci da taku, you no, zaku iya rayuwa da namiji tsawon shekaru ya Aureki Amma mu ba bahaushen da zai yarda irin hakan ya faru ke koda soyayya ce mai karfi watarana sai kin fuskanci damuwa, shine na gama karantar mazan bariki tun tuni namiji zaita kwashe mata yana cinyewa rana daya ya koma kauye ya Auro sweet sixteen, ke kinzama karuwa wannan yaci ya yar wancan yaci ya zubar, bakida value ko daraja wata rana ma aci a miki dukan tsiya,

Suzanne tace "you are right ki duba nida brown, ya Ajiyeni for years shima, kuma he is not ready to marry me saboda yafi son matar shi dani har fadamin yayi wai

bazai iya sakinta ba because shine first man a Rayuwar ta she is virgin, ko mu mazan mu sun san value na virgin girl,

Yanzu see me am here westing my time my opportunity my life, me nayi gaining a rayuwata? Nothing only insult sex stupid sex da dad'in shi na D'an lokacin da kukeyi ne da kun gama shikenan ko tuna me yafaru bazaki iya ba,

Sometimes zaizo sai muna cikin yi ya daga waya yace min inyi shiru matar shi ce kartaji muryar mace, ni kuma am such a fool da zaiyi waya da ita agabana yana mata hirar soyayya, Sofia now in zan samu miji zanyi Aure zanbar wannan Rayuwar da batada Amfani,

"Why not kibar shi tun yanzu ki koma karatun da kika jingine may be ki samu mijin Aure, Amma yanzu kina nan ana iki Kallon matar wani nan kuwa kina zaman karuwa ne,

Blessing ma magana tayi tareda rungume Sofia "Tanks to you friend Nima zan koma gida injira james if he truly want to marry me ya bini gida ya biya wani Abu akaina,

Zubaida Kara kuka tayi "na cuci kaina ni kam inada mai sona da zuciya daya na biyewa Aliyu gashi ya cuceni ya yaudare ni, "toh kibar shi da Allah ki gyara Rayuwar ki ki koma rayuwa a natse zakiga saka makon ubangiji, Allah zai baki wanda zai iya daukar ki a hakan cikin mutunci.

Tabasu shawar wari kuma da Alama sun dauka,

Bayan sati biyu ta kammala exam dinta wanda tayi bankwana da bariki tareda rabawa kawayen ta duk Abubuwan Amfanin su da bazata iya dauka ba, soba ta fara zuwa, domin yiwa baba yalwa Sallama domin sun cire komai sun rungume ta domin bata kulawa na matar ubansu, Bleesing ta fada mata sunyi engaged da james kuma zata gayyace ta suzo susha biki domin su ne dai kawayen nata, kuma tayi Alkwarin zuwa nan da wata hudu insha Allahu,

A zaune suke itada baba yalwa tana bata labari tana dariya ta kalleta ke kuwa Y'ar nan kina Kallon kanki kuwa? Kin koma kamar tsada gaki kinyi shar dake kodai ciki

kikeda shi? Zabura tayi tareda ja baya tana zare ido, wannan matar akwai fatan tsiya wallahi ina taga ciki ita uban wa ma zaiyi mata? "Y'ar nan fadamin gaskiya kodai kina bin maza ne a wurin karatu kinga yanda kika dashe kikayi tas tas ga wani kyau da kika Kara, nidai tun zuwan ki wancan satin nake kokonto,

Takasa cewa komai domin baba yalwa bakinta sam wani lokacin bai fadin Alkhairi inda sabo ta saba ma, yanzu ai wannan fatan tsiya ne,.

Karar wayar ta yasa tayi saurin dagawa, bakinta bai kumayi shiru ba duk da taga ta daga wayar tana kan cewa nidai ina ganin yaron ciki a jikin ki Safiya,

"Gaida momy tayi, momy tayi shiru tareda sauraran baba yalwa, "bawa babar ku wayar, mika mata tayi tareda cewa "ga momy na magana, karba tayi tana cewa " Hajiya Aisha Sannu, "yauwa yalwa ya gajiya? "Alhmdulillahi kina jina da Y'ar ki ko, inkin ga yanda ta koma dole kisata a daki ki bincike ta ta yi tas tas kamar tsada nidai inaga ciki takeda shi,

Katse ta momy tayi kawai tace "Dama na tabaki wayar ne domin mugaisa, zanma turo driver yau yadawo min da ita Abuja,

"Toh ku kaita Asibiti kuwa likita ya duba inkuma zubarwa zakuyi yafi rufin Asiri, a ce budurwa da ciki zamani ina zaka damu,

Karbar wayar ta tayi ta mike tana sauraran momy " get ready driver zaizo ku taho yau kinji, "tom momy tafada jikin ta a sanyaye, baba yalwa ta iya tada zaune tsaye wane irin ciki kuma?

Hada inata inata tayi karfe shabiyu driver ya iso suka Kama hanya, baccin ta ta sha har Abuja, saida suka shiga gari ta farka, tana tuna zuwan ta na farko, wani irin kewar shi takeji ko shi yana kewar ta?

A harabar gidan ta samu su twins suna ganin shigowar motar suka rugo suna jin dad'in ganin ta, "welcome back sister suka fada tareda karbar mata jakar ta,

Momy ta tarbeta itama cikeda murna " my house is complete now, "noo momy su yaya basu dawo ba, "yata ta dawo so am ok, bajewa sukayi suka kwashi dishes,

Sai dare Dady ya dawo da fada, ya kwalawa momy kira, Sunfito da murnar su suka gaida shi suka koma ido ya zubawa Sofia shima duk da baisan komai na canjin ciki ba yasan ta canja,

Tarar shi momy tayi tareda cewa "Dadyn yara lafiya? "Yalwa ta kirani tana fadamin. Mugun labari, a ranta tace wannan mata akwai tsegumi, "me tace maka? Kuma me ya faru? Ki bincika min Sofia in tanada ciki kamar y'anda yalwa ta fada in tana dashi kuwa I will find out who is responsible insa a hukunta shi hukunci mai tsanani,

"Koda D'an ka ne Alhaji? Tafada cikin Kallon tuhuma, da son ganin gaskiyar Abinda yake fada, "Abdul Rahaman? Yafada yana girgiza kai "yes koda shine ya mata cikin? " wait karki fadamin kinsani kuma gaskiya ne she is pregnant?

"Ban tabbatar ba Amma tunda ita munafuka ta fada maka inda cikin ba wanda zaka hukunta sai Abdul kuma in ma hakan ya faru kanada kaso babba a cikin al Amarin, na lallashe ka tun lokacin Abu bai kwabe ba ka Aura mai yarinyar kaki Aura mai, kace bakasan tushen taba, Alhaji ko karuwa a brothel ana Aurota ayi zaman Aure da ita indai zai haifarda da mai ido Amma lokacin kaki fahimta ta, nasan komai zai iya faruwa nayi ta binka ina lallashin ka Amma fur kaki fahimta ta, yau ya kake so muyi?

"So Aisha kina so kifada min Abdul Rahman ya gama lalata min yarinya kuna Kinada masaniya? Sannan kike kirarin naki Aura mai ita, toh Abdul Rahman zaizo ya sameni kuma bashi ba Sofia domin bazai taba Auren taba kuma cikin ni zan sa a cire mata shi Allah ne gatan ta nine gatan ta, kuma zai hadu da bacin rai na tunda Rayuwar banza ya dauka har yana iya yiwa wata mace ciki, to ya dawo na hafsat din ma na shine da kika daure mai kikace ba nashi bane.....

"Sorry for the typing error

Matar Soja[6/23, 1:20 PM] +234 806 628 8263: 63&64..... Dadyn twins ka natsu ka gano Abinda nake son nuna maka, wani lokacin muna saurin toshe barna mu iyaye idan munsa lura Amma wani lokacin muna sakaci naso kabi magana ta tun lokacin da yaron nan ya nuna maka yana bukatar Auren nan kuma yana kaunar Sofia naso ka saurare ni ka fahimci cewar komai na iya faruwa. "Wato so kike ki nuna min cewar ni bansan Abinda ya dace ba ko me? "Aa naso ka gano cewa akwai boyayyan Al amari a cikin soyayyar tasu tundaga lokacin da yabar gida na tsawon watanni har zuwa lokacin da nagano inda yake da kuma sanadin fitar shi wannan gidan cikin gatan shi haduwar shi da Sofia, sai na fawwala wa ubangiji Al amarin domin nasan komai nada sanadi yanada dalili, sannan zancen ciki inma ya tabbata ina so kasani ba acika son shishshigi a lamarin Aure ba musamman iyaye zamu iya hanawa barna ta bullo zai iya yuwuwa akwai rabo mai tsanani Amma muka bijire, kaga sai Abu ya lalace muzo muna da munsani, ni nasan hakan zai iya faruwa shiyasa nayiwa tufka hanci Sofia da Abdul Rahman ko ciki ne a tsakanin su na halas ne domin da igiyar Aure akan su,

Wani irin Kallon me kike nufi yake mata" yes nasa Andaura mai Aure domin nasan cewa akwai rawar kai da gajen hakuri a lamarin Abdul Rahman idan yana so baya tunanin right and wrong, kana ganin soyayyar hafsat da batakai ta Sofia ba yabar gidan nan just imaging abinda zaiyi akan soyayyar Sofia?

"Aisha wane irin Aure? Wane limamin ne ya daura Aure kamar wadda batada gata? Ok a tunanin ku tunda marainiyace shiyasa kuka tauye mata hakki kika bi son zuciyar yaronki kika bashi Auren ta, kinyi kuskure Aisha kinyi kuskure, kinyi Abinda ya nuna min cewar farin cikin D'an ki yafi komai, Kin aikata son ranki kin nuna selfishness because of your son happiness, ok ni kuma zan nuna muku iko, saboda ba Y'ar uwarki bace zaki bari ya Aureta ya cutar da ita harda ciki, kuma under my nose? Bata Auru ba ki fada mai tun kafin yadawo ya rubuta min sakin ta bazan bashi ya'ta ba ni yanzu zanfada kuma dole ku saurare ni ai haihuwar shi akayi ba shi ya haifemu ba, kuma keda duk wanda keda hannu sai ranku duka ya taru yafi nawa baci,. Tunda ya dauki fada bata ce uffan ba, zuba mai ido tayi kawai saida ya Ajiye tace "Dadyn twins, Abdul Rahman bai san da Aure a tsakanin su da Sofia ba haka itama Sofia batada labari, ina so kagano Abinda nake son nuna maka, yanzu da banyi..... Ya isheki Aisha kin gama nuna min kece mai ganewa ni bangane komai, ni kuma ina kokarin nuna miki shi yakama ta ya gane illar garaje ya rage hanzari ya jira lokacin da ya kamata ya ji maganar mu bamu zamuji tashi ba, wato Al adar ku ta banza bata fita a jikin ki ba ta bature domin mugun son ya'ya, Nima ina son Abdul Rahman Amma ba irin sonda zan biyewa son zuciyar shi ba, Alhmdulillah bai sani ba karku ma ki sake ya sanda hakan domin bazan taba bashi Sofia ba, ya gwada nashi iya shege yanzu zaiga nawa,

"Alhaji ka duba Al amarin nan kodan cikin da ake magana..... " sai kun cireshi a jikin yata, final, yafada tareda barin falon, zama tayi kan kujera tareda dafe kanta "INNALILLAHI WA INNA ILAIHIRRAJI UN, shine Kalmar da take mai maitawa domin wannan karon ne na farko da har mijin nata yake goran ta mata Al adar ta, tasan halin shi shiyasa ta ke tsoron fadamai tunfarko a tunanin ta gyara tayi batasan tayi laifi ba, kuma Allah yasani tana kaunar Sofia kamar twins ko Abdul Rahman, me ma zaisa ta kasa kaunar Abinda D'an ta keso, sannan yanzu gashi tana Y'ar uwar mijin ta, zataso ace Sofia is pregnant Amma saboda wannan fitinar jikin ta yayi sanyi,

Su Sofia na dakin su hankalin ta kwance domin tasan tana period kuma a sanin ta mace bazatayi ciki tana period dinta ba, canjin da ake ganin tayi ita tasan dalilin shi domin tasamu organic products masu inganci da tsada, wa inda sunyi matukar karbar ta tana jin dad'in jikinta itama fatar ta tayi laushi takara santsi, da komai nasu take amfani, sannan ga kwanciyar hankali, idan ta tuna yanzu gatan ta ya lunku sai farin cikin ta ya karu, duk shine ya tsolewa baba yalwa ido kuma don su momy basu san babatun ta bane shiyasa ita ai tasaba,,

Momy ce ta shigo fuskar ta kawai zata nuna maka tana cikin damuwa zama tayi tareda cewa twins su bata wuri, fita sukayi ba musu domin sun san Abinda ya dace, ba irin Y'an matan yanzu ba da sunfi karfin iyaye uwa nafada ya' nafada

Allah yasa mu dace ya kuma shirya mana zuri'a,

